daxin karanta Alqur'ani. A yanzu sun gano gaskiyar haxa son iyalan Manzo da son almajiransa.

Yi qoqari ka tsarkake zuciyarka, ka hutar da rayuwarka. Kada ka tsani ko wane musulmi balai sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Ya Allah kada ka sanya qyamar muminai a cikin zukatanmu. Ya Allah kai ne mai tausayi, mai jinqai.

Tsira da amincin Allah su daxa tabbata akan Manzonmu Muhammad da iyalansa da sahabbansa baki xaya.

Alhamdu Lillahi.

Fassara ta kammala a safiyar Jum'ah 1 ga Safar 1429 (8/2/2008) a Sakkwato.



# KYAKKYAWAR SAFIYA..

**(Cikakken Nazari Akan Matsayin Sahabbai A Lokacin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* Da Bayansa)**

**(صحبة الرسول بلغة الهوسا)**


NA

SHEIKH SALEH BIN ABDULLAH AL DARWISH

Alqali a kotun qoli ta Shari`ar Musulunci a Qaxif

(Qasar Saudiyyah)

Wanda ya fassara

Muhammad Mansur Ibrahim

Na Cibiyar Nazarin Addinin Musulunci

Ta jami`ar Usmanu Xan Fodiyo

SOKOTO

Bugu na farko an yi shi a 1429B.H/2008M

ISBN 978-2076-92-9

**© Haqqen buga wannan littafi na Mu'assasatu Ahlil Baiti Wassahabah, Najeriya ne.**
**Wanda yake son buga shi saboda Allah ya na iya tuntuvarmu a adireshinmu kamar haka:**
**Lamba 97, Titin Ahmadu Bello,**
**P.O.Box 2491,**
**Sokoto, Najeriya.**

**Ko kuma ya tuntuvi Mai Fassara a**
**mansursokoto@yahoo.co.uk**



Waxanne mutane ne suka rufa masa baya a wajen yaqoqan xaukaka addinin Allah?
Da wa yake shawarwari a lamurransa?
Su wane ne abokan cin abincinsa da sauran harkokinsa na yau da kullum waxanda hankalinsa yake kwantawa da zamansu a tare da shi?
Su waye ke sallah a bayansa, su saurari huxubarsa da wa'azojinsa?
Su wane ne ke kai masa ziyara? Shi ma idan ya tashi ziyara wurin su wa yake zuwa?
Wa ya bayar da dukiyarsa ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* don a taimaki addini?
Wa kuma ya sadaukar da rayuwarsa saboda shi?
Wane ne ya karvo mana saqon Allah daga wurinsa?
A gaban wa ne ya cika? Kuma wa ya yi masa wanka da sallah da jana'iza?
Wane ne ya gamu da baqin cikin rabuwa da shi ya yi kuka akan haka?

Babu shakka, wasu bayin Allah da ya nufe su da rabo suka tuba daga zagin sahabbai sun bayyana ni'imar da suka samu kansu a cikinta bayan tubansu. Sa'an nan ne suka fara sanin

zato ta zarce wannan wadda waxannan bayi suka samu?

Duk mai karanta Alqur'ani, ya yi nazarinsa da idon basira zai san cewa ba a tava cimma sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* wajen daraja da girma a wurin Allah da Manzo. Abin da wannan littafin ya qunsa tsokaci ne kawai kamar na mai xebo ruwa a bokiti daga gavar gulbi. Abin da bamu faxa ba na ayoyin Alqur'ani akan darajarsu idan ka duba Alqur'anin ka sa basirarka zaka gano shi. Muradi dai ka gane gaskiya, ka kuma tsaya akan ta, don kada wawaye su ruxe ka da an yi an ce.

**Kammalawa**

Tuna tsayawar da zaka yi a gaban Allah ranar alqiyama ya kai xan uwa. Sa'an na ka yi wa kanka waxannan tambayoyi domin amsar su za ta amfane ka in Allah ya so.

Sake nazarin dai ayoyin nan da ka karanta a wannan littafi da rayuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ga baki xayanta. Tare da wa ya yi ta?

Su wane ne xalibansa?



**BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM**
**GABATARWAR MAI FASSARA**

Godiya ta tabbata ga Allah. Tsira da aminci su tabbata ga Manzon Allah da iyalansa da sahabbansa baki xaya.

Shekaru kamar biyar kenan da suka wuce muka fitar da wani littafi mai suna "Alaqa tsakanin *Ahlulbaiti* da Sahabbai" wanda wani dattijo, malami kuma alqali a babbar kotun shari'ar Musulunci ta qaxif ya wallafa.

Na sanar da mai karatu yadda haxuwata da wannan bawan Allah ta kasance da yadda littafin ya shigo hannuna har na yi tunanin fassara shi domin amfanin makarantan Hausa.

Yau ma ga wani littafi nasa naga dacewar 'yan uwana musulmi masu magana da harshen hausa su amfana da shi. Kuma bai kasa wancan ga tarin ilmi da yawan fa'idar da ke cikinsa ba. Buqatar sanin irin waxannan littafai da fassara su a kullum daxa qaruwa take yi saboda tallata varna da ake yi a cikinmu dare da rana.

Allah ya sa wannan littafi ya biya buqatar da aka yi shi domin ta.

Baban Ramla,
Muhammad Mansur Ibrahim Sokoto

## BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM

## GABATARWAR MAI LITTAFI

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah wanda tsarki ya tabbatar masa. Muna neman gafararsa, muna tuba zuwa ga reshi, muna kuma neman tsarin Allah daga sharrurrukan kawunanmu da na miyagun ayyukanmu. Duk wanda Allah ya shirye shi wannan shi ne shiryayye. Wanda kuwa duk Allah ya vatar da shi to, babu wanda ya isa ya shirye shi.

Bayan haka, Allah a cikin ikonsa ya kawo mu lokaci wanda musulmi muka fara faxaka, muka fara sanin ciwon kanmu bayan mun sha wuya mai yawa a hannun kafirai waxanda a kullum neman su ke su durqusar da mu. Ba wani abin da zai taimake mu akan ci gaba da samun nasara kamar haquri da sanya tsoron Allah a gaba. Domin su biyun su ne jigon duk wata nasara da xaukakar da mu ke nema.

Rabuwar kan da musulmi mu ke fama da ita tana yi wa maqiyanmu daxi matuqa. Tana kuma taimaka masu wajen karya qarfinmu da yin barazana a gare mu.



Ga wata ayar kuma:

﴿ فَبِمَا رَحۡمَةٖ مِّنَ ٱللَّهِ لِنتَ لَهُمۡۖ وَلَوۡ كُنتَ فَظًّا غَلِيظَ
ٱلۡقَلۡبِ لَٱنفَضُّواْ مِنۡ حَوۡلِكَۖ فَٱعۡفُ عَنۡهُمۡ وَٱسۡتَغۡفِرۡ لَهُمۡ
وَشَاوِرۡهُمۡ فِي ٱلۡأَمۡرِۖ فَإِذَا عَزَمۡتَ فَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ
يُحِبُّ ٱلۡمُتَوَكِّلِينَ ١٥٩ ﴾ آل عمران: ١٥٩

**Ma'ana:**

Saboda wata rahama ce daga Allah ka yi sanyin hali a gare su. Kuma da ka kasance mai hushi, mai kaushin zuciya, da sun watse daga gefenka. Sai ka yafe musu laifinsu, **kuma ka nema musu gafara,** kuma ka yi shawara da su a cikin al'amarin. Sa'an nan kuma idan ka yi niyyar zartarwa, to, ka dogara ga Allah, lalle ne, Allah yana son masu tawakkali.

Suratu Ali Imran: 159

Manzo xin da kansa ne aka ce ya shawarce su duk da kasancewar Allah ke aiko masa saqo dare da rana. Ga kuma neman gafarar da aka ce ya yi masu. Ka fahimci saqon? Wace daraja kake

سُوقِهِۦ يُعۡجِبُ ٱلزُّرَّاعَ لِيَغِيظَ بِهِمُ ٱلۡكُفَّارَۗ وَعَدَ ٱللَّهُ

ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ مِنۡهُم مَّغۡفِرَةٗ وَأَجۡرًا

عَظِيمَۢا ﴿٢٩﴾ الفتح:٢٩

**Ma’ana:**

Muhammadu manzon Allah ne. Kuma **waxannan da ke tare da shi** masu tsanani ne a kan kafirai, masu rahama ne a tsakaninsu, ka na ganinsu suna masu ruku'i masu sujada, suna neman falala daga Ubangijinsu, da yardarsa. Alamarsu tana a cikin fuskokinsu, daga kufan sujuda. Wannan ita ce siffarsu a cikin Attaura. Kuma siffarsu a cikin Linjila ita ce, kamar tsiron shuka wanda ya fitar da reshensa, sa’an nan ya qarfafa shi, ya yi kauri, sa’an nan ya daidaita a kan qafafunsa, yana bayar da sha’awa ga masu shukar, domin (Allah) ya fusatar da kafirai game da su. Kuma Allah ya yi alqawali ga waxanda suka yi imani kuma suka aikata ayyukan qwarai



Idan muka yi duba da kyau zamu ga cewa, riwayoyin qarya da suka zo mana na tarihi waxanda aka kyautata adonsu, aka shafa masu kwalli, aka qamsashe su da turare na daga cikin abubuwan da ke qara samar da tazara a tsakaninmu. Abin da maqiyanmu suke daxa zuga shi suna rura wutarsa. Duba yadda aka faxaxa savanin da ya gudana a tsakanin mutane bayan wafatin Manzon Rahma *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Kai ka ce wasu irin mutane ne ake ba ka labarinsu waxanda ba su ko tava jin qamshin musulunci ba ballantana a ce sun zauna da Manzo kuma su ne almajiransa, abokansa, surukansa, mataimakansa, waxanda a tare da su ne ya yi gwagwarmayar kafa musulunci, kuma su ne suka tsare masa addinin a bayansa, suka ci gaba da yaxa shi har ya game duniya!

Alhaki ne mai nauyin gaske akan malamai da masana su bayyana gaskiya a ko wane lokaci, ina ma a irin wannan?

Wannan xan littafi ya zo ne don ya janyo hankalin ‘yan uwa musulmi maza da mata don koma ma turba, da gane gaskiya wacce zamu ganta a cikin bayanin Allah da na Manzonsa. Haka kuma littafin ya qunshi bayanai na hankali

waxanda duk mai basira ba ya tantama akan sahihancinsu. Muradina shi ne bayyana gaskiya. Idan na dace na gode Allah, wanda kuma daga wurinsa na ke neman gafarar zunubaina baki xaya.

Xan uwa mai karatu, ga ka ga littafin. Idan ka ga wasu shawarwari masu amfani ko wata suka mai ma'ana kar ka kevanta da su. Ka aiko su kai tsaye don nasiha ga al'umma. Allah ya sa mu zan cikin masu gyara.

Salihu xan Abdullahi Ad Darwish

A qasar Saudiyyah



Abin da ya kamata mu sani anan shi ne cewa, sahabbai hawa hawa ne. Ko waxanne daga cikinsu na da matsayi da martaba ta musamman. Amma wasu na gaban wasu. Sahabban da suka je yaqin raba gardama (Badar) da yaqin ramuwar gayya (Uhud) da yaqin qare dangi (Khandaq) da masu mubaya'a a qarqashin itaciya su ne mafi daraja daga cikin sahabbai.

Ka ga dai Allah ya yaba wa waxanda suka je yaqin Tabuka. Waxanda shaixan ya qawata masu rashin tafiya kuma suka yi nadama su kuma Allah ya yafe masu. Sai kuma waxanda rauni da sauran uzura suka hana su zuwa su kuma Allah ya faxi hanzarinsu. Abin da ya rage shi ne kawai munafukai. To, me zaka ce ga wanda ya haxe duka waxannan kason ya soke su baki xaya? Ai wannan iyakar wauta da jahilci kenan.

**Daga qarshe..**

Mu saurari wani kira na maxaukakin sarki zuwa ga Manzonsa.

﴿ وَٱصۡبِرۡ نَفۡسَكَ مَعَ ٱلَّذِينَ يَدۡعُونَ رَبَّهُم بِٱلۡغَدَوٰةِ وَٱلۡعَشِيِّ يُرِيدُونَ وَجۡهَهُۥۖ وَلَا تَعۡدُ عَيۡنَاكَ

qasa ta yi qunci akansu duk da yalwantar ta. Kuma rayukansu suka yi masu qunci, kuma suka tabbata babu wata mafaka daga Allah sai (komawa) zuwa gare shi. Sa'an nan Allah ya karvi tubansu, (ya basu iznin) su yi tuban. Lalle Allah ne mai karvar tuba, mai jinqai. Ya ku waxanda suka yi imani! ku ji tsoron Allah, kuma ku zamo tare da gaskiya.

Suratut Taubah: 117-119

Annabi da Muhajiruna da Ansar, Allah ya yi tuba akansu don jinqansa a gare su. Sauran ukun da basu halarci yaqin ba kuma sun yi nadama su ma Allah ya yafe masu. To, gaya min wa ya rage kenan? Saura munafukai aka riga aka tona asirransu. Ko kaga wata aya a Alqur'ani wadda ta soki Muhajiruna da Ansar?

Ka tuna magabatan da aya ta faxa can da farko waxanda Allah ya ce ya yarda da su. Su wane ne? Duk wanda ya yi sallah a alqibla biyu yana cikin magabata. Haka ma duk wanda ya yi mubaya'a a lokacin hudaibiyyah yana cikin magabata.



**Da Me Aka Aiko Manzo?**

Tun da farko bari mu fara nazarin waxannan ayoyi:

قَالَ تَعَالَى: أَعُوذُ بِٱللَّهِ مِنَ ٱلشَّيْطَٰنِ ٱلرَّجِيمِ ﴿ رَبَّنَا وَٱبْعَثْ فِيهِمْ رَسُولًا مِّنْهُمْ يَتْلُوا۟ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتِكَ وَيُعَلِّمُهُمُ ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْحِكْمَةَ وَيُزَكِّيهِمْ ۚ إِنَّكَ أَنتَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿١٢٩﴾ ﴾ البقرة: ١٢٩

**Ma'ana:**

Ya Ubangijinmu ka aiko da **Manzo daga cikinsu** wanda ya ke karanta masu ayoyinka, kuma ya sanar da su littafin (Alqur'ani) da Hikima (Sunnah) kuma ya tarbiyyantar da su. Domin lalle Kai ne gwani, Mai hikima.

Suratul Baqara: 129

﴿ هُوَ ٱلَّذِى بَعَثَ فِى ٱلْأُمِّيِّـۧنَ رَسُولًا مِّنْهُمْ يَتْلُوا۟ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتِهِۦ وَيُزَكِّيهِمْ وَيُعَلِّمُهُمُ ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْحِكْمَةَ وَإِن كَانُوا۟ مِن قَبْلُ لَفِى ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿٢﴾ ﴾ الجمعة: ٢

**Ma'ana:**

(Allah) Shi ne wanda ya aiko da Manzo a cikin ummiyawa yana karanta masu ayoyinsa kuma ya tarbiyyantar da su, ya kuma karantar da su littafin (Alqur'ani) da Hikima (Sunnah), duk da

ya ke sun kasance a cikin bayyanannen vata can gabanin haka.

Waxannan ayoyin a sarari sun nuna irin alaqar da ke tsakanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da sahabbansa. Waxannan ayyukan da aka zayyana kuma su ne muhimman wajibai da Allah ya xora masa don ya tsayu da su. Kuma ko shakka babu ya yi iya qoqarinsa wajen sauke wannan nauyi. Saboda haka Allah ya taimake shi ya fitar da mutane daga vata zuwa shiriya, daga kafirci zuwa miqaqqiyar hanyar Tauhidi.

Duba yadda Allah ya ce, “Manzo daga cikinsu”. Daga cikinsu ne Manzon Allah ya fito. Ya rayu a Makka tsakanin jama’arsa, duk rassan quraishawa danginsa ne. Ko mutanen Madina ma *Banun Najjar* danginsa ne, kawunnen kakansa Abdul Muxxalib.

Allah ya zavar wa Manzonsa dangi ‘yan girma, ya fitar da shi daga zuri’ar Annabi Ibrahim *Alaihis Salam* kuma ya aiko shi a Makka, garin da yafi ko wane gari daraja a bayan qasa. Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne addu’ar kakansa Ibrahim ta faxa akan sa, kuma



بَعۡدِ مَا كَادَ يَزِيغُ قُلُوبُ فَرِيقٖ مِّنۡهُمۡ ثُمَّ
تَابَ عَلَيۡهِمۡۚ إِنَّهُۥ بِهِمۡ رَءُوفٞ رَّحِيمٞ ﴿١١٧﴾ وَعَلَى
ٱلثَّلَٰثَةِ ٱلَّذِينَ خُلِّفُواْ حَتَّىٰٓ إِذَا ضَاقَتۡ عَلَيۡهِمُ ٱلۡأَرۡضُ
بِمَا رَحُبَتۡ وَضَاقَتۡ عَلَيۡهِمۡ أَنفُسُهُمۡ وَظَنُّوٓاْ أَن لَّا
مَلۡجَأَ مِنَ ٱللَّهِ إِلَّآ إِلَيۡهِ ثُمَّ تَابَ عَلَيۡهِمۡ لِيَتُوبُوٓاْۚ إِنَّ
ٱللَّهَ هُوَ ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ ﴿١١٨﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَكُونُواْ مَعَ ٱلصَّٰدِقِينَ ﴿١١٩﴾ ﴾ التوبة:
١١٧ - ١١٩

**Ma’ana:**

Lalle ne, Allah ya yi tuba akan Annabi da Muhajiruna da Ansar waxanda suka bi shi, a cikin lokacin tsanani, daga baya zukatan wani vangare daga gare su sun yi kusa su karkata, sa’an nan (Allah) ya yi tuba akan su. **Lalle Shi ne mai tausayi, mai jinqai a gare su**. Kuma (Allah) ya karvi tuban mutane ukun nan waxanda aka jinkirtar (aka hana mutane yin magana da su) har

uku su ne waxanda suka yi imani da Allah da ranar lahira, kuma suke bada dukiyoyinsu don neman kusanci zuwa ga Allah da samun addu'oin Manzon Allah.

Sai labarin waxanda suka qi fita yaqin Tabuka, su ma Allah ya fayyace labarinsu. Sun yi furuci da laifinsu, don sun haxa aikin qwarai da mugun aiki amma suna neman tuba daga Allah kuma Allah zai karvi tubansu don Shi mai gafara ne, mai jinqai.

Waxanda basu je yaqin Tabuka ba sanannu ne a munafucci ba wanda ya damu da su, kuma sun kawo uzurran qarya sun gwada ma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Amma Allah ya san abin da suke ciki kuma ya bayyana ma muminai. Sai dai mutane uku kawai waxanda su a cikin sahabbai suke ba a cikin munafukai ba, ba kuma a cikin qauyawa masu raunin imani da jahilci ba. Shexan ya yi masu aiki. Basu fita jihadi ba bisa ga rashin dalili. Sun yi laifi a wurin Allah. Amma saurari dokar da ta fito daga maxaukakin sarki bayan qare yaqin.

﴿ لَقَد تَّابَ ٱللَّهُ عَلَى ٱلنَّبِيِّ وَٱلْمُهَٰجِرِينَ
وَٱلْأَنصَارِ ٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوهُ فِي سَاعَةِ ٱلْعُسْرَةِ مِنۢ



shi ne shugaban 'yan adam baki xaya. Shi ne kuma mai fitaccen matsayi a alqiyama, mai tafkin alkausara, mai matsayi mafi xaukaka da ceto mafi girma. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne mafificin mutane kuma jagoran Annabawa da Manzanni baki xaya.

Yana daga cikin ni'imomin da Allah ya yi wa Manzonsa kasancewar ya zavar masa abokan zama na kirki, masu fahimta da himma da jarunta. To, ina abin mamaki a nan? 'Yan uwansa ne na jini da tsoka, kuma su ne waxanda suka fi kowa tsarki a dangartakarsu da halayensu. Kamar yadda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce, "Mutane kamar ma'adinai ne. Zavavvunsu a jahiliyyah su ne zavavvunsu a musulunci idan sun ilmantu".[1]

A wani hadisin kuma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya bayyana zavin da Allah ya yi wa kakansa kinanata daga cikin 'ya'yan Ismail *Alaihis Salam*, sannan da zavin da ya yi wa quraishawa daga cikin zuri'ar kinanata. Daga cikin quraishawan ma sai Allah ya zavi Banu Hashim. Sannan daga cikinsu ne Allah ya zavi

[1] Duba Sahihul Bukhari (6/298) da Sahihu Muslim, Hadisi na 2526.

Manzonsa *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Don haka a tare da su ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya gamu da wahalhalun da suka haxa da yanke hulxar da larabawa suka yi masa na tsawon lokaci. Kuma su xin dai ne *Ahlulbaiti* waxanda Allah ya haramta masu cin sadaqa saboda kusancinsu da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Xan uwa! sake nazarin ayoyin da suka gabata. Allah fa ya ce Manzonsa ya tarbiyyantar da su. To, zamu zo mu yi suka ga tarbiyyar tasu? Duba yadda ya gabatar da tarbiyyarsu akan ilmantar da su. Ko saqon ya isa da kyau ga reka?

Allah Ta'ala ya ce, Annabinsa ya karantar da su littafi. Akwai mai hankali da zai iya cewa su jahilai ne?

Bayan da Allah Ta'ala ya qarasa wannan bayani a Suratul Jum'ah sai kuma ya ce:

﴿ ذَٰلِكَ فَضۡلُ ٱللَّهِ يُؤۡتِيهِ مَن يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ ذُو ٱلۡفَضۡلِ ٱلۡعَظِيمِ ٤ ﴾ الجمعة: ٤

**Ma'ana:**

> Waccan falalar Allah ce da ya ke bayar da ita ga wanda ya so. Kuma Allah Mai falala ne babba.



qarshe qarshen surorin da suka sauka domin bayan cin garin Makka ne ta sauka.

Wannan sura ta Taubah ta fayyace yanayin al'ummar birnin Madina a wannan lokaci. Surar sai da ta fayyace labarin munafukai daki daki, ta bayyana siffofinsu da xabi'unsu. Allah ya faxi yadda wasu mutanen birni suka goge ga munafucci kuma idan aka shelanta jihadi sai su rafashe su daqushe mutane. Idan kuma aka nemi agaji na kuxi basu bayarwa. Waxanda ke bayarwar kuma munafukai sai sun yi zunxensu. Allah ya bayyana munafukai masu son kai ne da rantsuwar qarya da yaxa jita jita.

Kwatanta siffofin munafukai a wannan sura da siffofin magabatan musulmi da Allah ya bayyana. Kai kaga manyan sahabbai na cikin waxanda munafucci ya shafa?

To, sai labarin mutanen qauye. Surar ta kasa su kashi kashi. A cikinsu akwai masu tsananin kafirci da munafucci da waxanda suka jahilci iyakokin Allah. A cikinsu akwai masu bayar da dukiyarsu ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* suna ganin kamar an xora masu tara. Irin waxannan jira kawai su ke wata musiba ta cimma musulmi su ji daxi. Kashi na

Abubakar ya ziyarce ta tare da Umar *Raliyallahu Anhum*.

Sake komawa a cikin ayoyin, duba yadda Allah ya ce ya qawata masu imani ya sanya masu sonsa. Ya qyamatar da kafirci da fasiqanci da savo a ga resu. Duka wannan kuma falala ce da ni'ima daga wurinsa. Sai kuma a qarshen ayar ya ce, su ne shiryayyu. Gaya min wasu mutane irin waxannan masu katin shaida irin wannan!

Abdullahi xan Mas'udu *Raliyallahu Anhu* ya yi gaskiya da ya ce, Allah ya duba zukatan bayi sai ya samu zuciyar Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* tafi ta kowa tsafta, sai ya zave shi ya aiko shi da manzanci. Sa'an nan ya duba zukatan sauran jama'a sai ya samu sahabban Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* sun fi kowa tsarkin zukata sai ya haxa su da shi suka zamo mataimakansa kuma abokan shawararsa.

**Yaqin Tabuka**

Allah Ta'ala ya saukar da Suratut Taubah don bada labarin wannan yaqi tun daga dalillan da suka janyo shi har zuwa yadda ya faru da kuma darussan da ke cikinsa. Surar tana cikin



Babu shakka zama sahabin Manzo ni'ima ce babba kuma falala ce daga Allah. Waxanda suka same ta kuwa Allah ne ya zave su da ita ya fifita su akan saura.

Babu shakka kuma cewa, dangantakar da ke tsakanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da sahabbansa dangantaka ce mai qarfi mai albarka. Daga cikinsu ko har da iyalansa waxanda suka haxa da matansa iyayen muminai. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* yana murna da kasancewarsa tare da su. Su ne rundunarsa, su ne almajiransa, su ne mataimakansa. A tare da su ya rayu, kuma a cikinsu ya cika. Haka kuma su ne suka xauko mana saqonsa ta hanyar kiyaye alqur'ani da Sunnah har suka hannunta su ga Tabi'una na bayansu.

Don haka duk mai son Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* wanda ya ke ganin girmansa, ya kuma yarda da cewa, ya isar da saqon ubangijinsa ya sauke nauyin da aka xora masa to, ya yarda da cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya karantar da su, ya horar da su akan tarbiyya ta gari. Duk wata sukar da mutum zai yi a gare su to, babu shakka

suka ce ga mai gidansu kuma malaminsu *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Ka mayar da hankali ka gani wane ne ya kamata a soke shi, sahabban Ma'aiki *Sallallahu Alaihi Wasallama* ko wanda ya ke sukarsu?

Bari in ba ka qaramin misali. Ya kake ji idan wani sarki ko shugaban qasa ko jagoran wata al'umma wanda su ke ji da shi, wanda kuma ya kafa wata aqida ko siyasa ko wani ra'ayi mai tasiri, sai aka sami wasu masu cewa su mabiyansa ne amma kuma sai suna sukar makusantansa da 'yan majalisarsa da abokan shawararsa da surukansa, sai suna cewa, duk 'yan iska ne suke tare da shi 'yan abi sabon sarki don a sha kixa? Kuma suna qarawa da cewa ai duk mayaudara ne masu son ya mutu su kafa kawunansu? Alhali kuwa su ne suka sayar da rayukansu wajen ganin aqidarsa da ra'ayoyansu sun kafu, bayan haka kuma suka yaxa su a duniya?

Me zaka ce kuma idan wannan shugaban dai ya fito fili ya yaba ma makusantan nasa yabo wanda ya kai matuqa, sannan ya kushe ma maqiyansu da duk mai raina al'amarinsu da qoqarinsu?



wannan baiwa, Sahabbai kenan) su ne shiryayyu. Falala ce da ni'ima daga Allah. Kuma Allah mai yawan sani ne, Gwani.

Suratul Hujurat: 7-8

Duba wannan irin alaqa tsakaninsu da Manzo. Ku sani Manzon Allah yana a cikinku. A cikinsu ya ke safiya da marece. Su ne abokan hulxarsa ta ko wace fuska. Su kaxai ne idan yace *Sami'allahu Liman Hamidu* zasu ce *Allahumma Rabbana Wa Lakal Hamdu*. Ga resu yake aure, ga resu yake aurarwa. Ga resu yake saye, ga resu yake rance, wurinsu yake neman shawara, da su yake sa wa da fitarwa.

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuma har wayau shi ne alqali mai yanke hukunci a al'amurran da suka shafi rayuwarsu har ga abinda ke tsakaninsu da iyalansu. Kuma sau da yawa wahayin ne yake sauka ya warware masu matsalolinsu idan sun tuntuvi Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* kamar yadda ya faru a labarin Khaulatu wanda ya zo a Suratul Mujadala.

Ba mamaki idan Ummu Hani tayi kuka akan yankewar wahayi a lokacin da sayyiduna

abin da qauyawa suke yi masa na kausasa murya a wajen magana da Manzon Allah kamar yadda suka saba yi wa junansu. Su ma qauyawan sahabbansa ne amma wa ya iya raba jemage da cin kaxe?

Sai kuma babbar ni'imar da Allah ya janyo hankalinsu zuwa ga reta.

﴿وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ فِيكُمۡ رَسُولَ ٱللَّهِۚ لَوۡ يُطِيعُكُمۡ فِي كَثِيرٖ مِّنَ
ٱلۡأَمۡرِ لَعَنِتُّمۡ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ حَبَّبَ إِلَيۡكُمُ ٱلۡإِيمَٰنَ وَزَيَّنَهُۥ فِي
قُلُوبِكُمۡ وَكَرَّهَ إِلَيۡكُمُ ٱلۡكُفۡرَ وَٱلۡفُسُوقَ وَٱلۡعِصۡيَانَۚ أُوْلَٰٓئِكَ
هُمُ ٱلرَّٰشِدُونَ ٧ فَضۡلٗا مِّنَ ٱللَّهِ وَنِعۡمَةٗۚ وَٱللَّهُ
عَلِيمٌ حَكِيمٞ ٨﴾ الحجرات: ٧ - ٨

**Ma'ana:**

Kuma ku sani fa lalle Manzon Allah yana a cikinku. Da yana bin ku ga al'amurra da yawa da kun wahala. To, amma sai **Allah ya soyar da imani a ga reku**, kuma ya qawata shi a cikin zukatanku, kuma ya qyamatar da kafirci da fasicci da savo zuwa ga reku. Waxannan (da Allah ya yiwa



Akwai shugaban da ya ke jin daxi a soki 'yan majalisarsa da makusantansa a ce duk macuta ne?

Me zaka ce game da malamin da ya qare rayuwarsa wajen karantar da xalibansa waxanda su kuma suka yi haquri da shi a ko wane hali har da yaqar iyayensu da danginsu suka yi akansa kuma suka qaurace ma gidajensu da qasarsu suka sadaukar da dukiyarsu akansa. Sai kuma ga wasu mutane a bayan wucewarsu suna sukar su, suna jifar su da jahilci da son rai da voye karatu?

Ya zaka sifaita matsayin wannan malami a idon masu sukar almajiransa? Kuma shi malamin ya kake ganin ra'ayinsa akan waxannan mutane?

Wane ne ya cancanci a soki lamirinsa, malam da ya yi qoqarinsa ko almajirai da suka sadaukar da lokacinsu da dukiyarsu har ma da jinainansu? Ko kuwa dai mai sukar lamirinsu ne ya cancanci a soke shi?

Xan uwana mai karatu! Duba fa ka gani.. Wannan fa Manzon Allah ne mai girma, jagoran masu faxakarwa da lurarwa. Sahabbansa kuma su ne suka dage a wajen taimakonsa da daxi ba daxi har ta kai ga yaqi mai tsanani amma ba su canza sheqa suka bar shi ba. Sun mutunta

zancensa, sun yi koyi da aikinsa. Su ne suke tsera da junansu wajen shan sauran ruwan alwalarsa da majinar da ta fito daga hancinsa mai tsarki. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuma ya bi dukkan hanyoyi da dabaru na koyarwa da bada tarbiyyah akan su. Ya kira su gaba xaya, ya lurar da su a xaixaiku. Ya kan yaba ma wanda ya yi daidai, ya gode ma wanda ya kyautata. Duk abin da ya ke alheri a ga resu ya nuna masu shi. Abin da ya ke akasin haka ko ya tsoratar da su daga yin sa.

Ya ma zamu iya sifaita aikin wannan malami a wannan xan qaramin littafi? Kuma wai duk da haka a ce aikin nan nasa bai yi amfani ba domin wai gungun shashashu kawai ya tara waxanda mutuwarsa ke da wuya suka ja da baya suka hau dokin zuciya suka hole ma rayuwarsu kuma wai suka sayar da addininsu da ‘yan kuxi kaxan! Wa ya karvi kuxin? Wa ma ya bayar da su? Daga ina suka fito? Ko kuma wai suna neman girma!! Wane girma ya kai ga nasu, su da suke sahabban mafi daraja ko a annabta?

Ban san dalilin da mai sukarsu zai iya kawowa domin hankali ya natsu da shi ba wanda zai sa su yi ridda bayan duk wahalhalunsu da



To, duba qarshen ayar. Allah ya yi alqawali ga waxanda suka yi imani kuma suka aikata ayyukan qwarai daga cikinsu da gafara da lada mai girma.[4]

Ina ba ka shawarar ka karanta Suratul Hujurati don samun qarin haske game da matsayin sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a wurin ubangijinsu.

Bari mu duba wurare biyu daga cikin surar don samun haske bisa bayanin da muke akan sa:

## Matsayin Sahabbai A Suratul Hujurati

A farkon surar dai Allah ya fara da kiran muminai su gabatar da Allah da Manzo a cikin ko wane sha’ani, kada su rinqa gaggawar bada shawarwari da ra’ayoyansu har sai sun samu umurnin Allah. Sai wani kyakkyawan ladabi da Allah ya koya masu na sassauta murya idan suna magana da maigidansu Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Yi nazarin banbancin ladubban da Allah ya koya ma sahabbai da kuma

[4] Daga cikinsu ba yana nuna sashensu kawai ke da wannan falala ba kamar yadda faxar Allah cewa, “Ku qaurace ma qazanta daga gumaka” ba tana nuna sashen gumaka kawai ke da qazanta ba.

sahabban Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Ga siffofinsu nan cikin Attaura da Linjila. Tirqashi! Lallai kam na gaba ya yi gaba, na baya ko sai biyar sau in yana rabo.

Yi kyakkyawan nazari a cikin siffofin.

1. Masu tsanani ne ga kafirai
2. Masu rahama ne a tsakanin su (musulmi)
3. Suna yawaita ibada musamman ruku'i da sujada (Suna Tawali'u)
4. Suna neman falala da yardar Allah (Ikhlasi)
5. Suna da alamar kwarjini a fuskokinsu
6. Suna da kama da tsire qasaitacce mai ban sha'awa
7. Suna baqanta zukatan kafirai idan sun dube su.

Ko ka fahimci saqon? Ko dai har yanzu kana nan kana maimaita qarairayin tarihi da basu da kai balai kayan xorawa?

Suna da kama da tsire wanda ya ke farawa qarami yana girma a hankali. Wa ya shuka tsiren? wa ya ba shi ruwa? wa ya kula da shi har ya qasaita ya zamo abin shawa? Idan ka kushe ma wannan shuka to, har manomin ma ai ba zaka bari ba.



faxi tashinsu na ganin tsayuwar addini da taimakon jagora *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Zai ce imaninsu ba ya da qarfi ne? Ko kuwa sun gagari mai tarbiyyar ne har ta yadda ba ya iya gyara su? Ko yana ganin aibin na malamin ne shi ne ya kasa? Ban sani ba.. wace amsa ce take masa daxi!

Duba a hankali.. Sun yi jihadi da haquri. Sun abokanci Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* a duk in da ya ja daga da maqiyansa. Sun yi jihadi da rayuwa, sun yi da dukiya, sun yi da fatar baki. Sun yi tsera a duk ayyukan alheri har sai da suka cimma buqata, suka kai matsayin da Allah ya ce ya yarda da su.. sa'annan kuma wai suka ja da baya suka sauya ra'ayi! *Inna lillahi Wa Inna Ilaihi Raji'un*.

Dukkanmu mun yarda cewa dai shi Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi iyakar qoqarinsa. Bai kasa ba, bai yi rauni ba. To, idan har muka mayar da kasawar ga mabiyansa, muka ce taron mayaudara ne ai har wayau mun yi suka akansa, musamman idan muka yi la'akari da cewa su ne makusantansa abokan shawararsa waxanda suke kewaye da shi dare da rana kamar munduwa.

Me yasa ba zamu yi tunanin mai kawo labarin shi ke da matsala ba? Ga wani misali:

Masana tarihi duka sun haxu akan cewa, wata qungiyar a ware ta fita daga cikin rundunar sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* waxanda kuma aka san su da sunan *Khawarij*. Ali *Raliyallahu Anhu* ya yaqe su da kansa daga bisani saboda irin ta'addancinsu da cin zarafinsu ga musulmi har ma sun kashe sahabin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba tare da wani laifi ba. To yanzu shi kenan sai mu ce bayyanar wannan qungiyar laifin Sayyidina Ali ne? Ko kuwa sai mu zargi dukkan magoya bayansa da makusantansa? Sai mu ce duk waxanda suka yi masa mubaya'a kafirai ne azzalumai ko fasiqai ne jahilai? Zamu yi haka akan kawai wata qungiya wadda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya bada labarin vullarta da haxarinta da ta'addancinta?

A ganina wanda ya ke irin wannan tunani ya kamata a tuhumci tunaninsa maimakon tuhumar barrantattun mutane.

To, idan ko haka ne ai mun sani Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne yafi cancanta mu kare shi. Haka ma jama'arsa da



daga cikinsu da gafara da lada mai girma.

Suratul Fathi, Aya ta 29.

Wannan ayar qarara ta nuna mana cewa, Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne mafifici a cikin annabawa, sahabbansa kuma su ne mafifita akan sahabban sauran annabawa. A maimakon a faxe su da sunan sahabbai sai aka ce, waxanda ke tare da shi. Me ka fahimta a nan? Suna tare da shi da zukatansu, da jikinsu da qoqarinsu. Suna tare da shi a aqidarsa da addininsa da gwagwarmayarsa. Suna tare da shi a duk in da ya nufa da duk in da ya sa kansa in zaman lafiya in yaqi. Suna tare da shi a duk matakin da ya xauka ba su sava masa. Suna tare da shi sun bar iyayensu da danginsu da abokanensu duk da suka sava masa. Suna tare da shi a lokacin daxi da na xaci, sauqi da wahala ba su rabuwa da shi. Taren tana da faxi sosai. Sirrin Alqur'ani kuwa na zavin kalmomin da suka dace da sanya su in da ya dace sai mu ce *Ma Sha Allahu*.

Sai kuma siffofinsu. Gasu nan Alqur'ani ya zayyana. Abin tubarkallah. To, ba anan kawai ba har cikin littafan magabatan annabawa an faxi

سُوقِهِۦ يُعۡجِبُ ٱلزُّرَّاعَ لِيَغِيظَ بِهِمُ ٱلۡكُفَّارَۗ وَعَدَ ٱللَّهُ

ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ مِنۡهُم مَّغۡفِرَةٗ وَأَجۡرًا

عَظِيمَۢا ﴿٢٩﴾ الفتح:٢٩

**Ma’ana:**

Muhammadu manzon Allah ne. Kuma **waxannan da ke tare da shi** masu tsanani ne a kan kafirai, masu rahama ne a tsakaninsu, ka na ganinsu suna masu ruku'i masu sujada, suna neman falala daga Ubangijinsu, da yardarsa. Alamarsu tana a cikin fuskokinsu, daga kufan sujuda. Wannan ita ce siffarsu a cikin Attaura. Kuma siffarsu a cikin Linjila ita ce, kamar tsiron shuka wanda ya fitar da reshensa, sa’an nan ya qarfafa shi, ya yi kauri, sa’an nan ya daidaita a kan qafafunsa, yana bayar da sha’awa ga masu shukar, domin (Allah) ya fusatar da kafirai game da su. Kuma Allah ya yi alqawali ga waxanda suka yi imani kuma suka aikata ayyukan qwarai



suka abokance shi da iyalansa da suke danganta zuwa gare shi kuma suka taimake shi duk sun fi cancanta da samun irin wannan kariya daga gurvataccen tunani irin na wawaye.

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* dai shi ne malami a yayin da sahabbansa suka kasance su ne xalibai masu karatu a gabansa. A cikinsu ko har da iyalansa masu tsarki. Shi ne kuma Jagora a lokacin da sahabbai su ne mayaqan musulunci da ke tafiya da umurninsa. A cikinsu har da iyalansa masu tsarki. Shi ne kuma mai tarbiyya a lokacin da sahabbai su ne al’ummar da yake reno da nagartacciyar tarbiyyarsa. A cikinsu kuwa har da iyalansa masu tsarki. Haka kuma shi ne sarki wanda daga cikin sahabbai ne ya ke da mataimaka da abokan shawara da ma’aikata da gwamnoni da surukai da maqwauta. A cikin su ko har da iyalansa masu tsarki. Qarawa da qarau shi manzo ne wanda sahabban nan dai su ne ya isar ma manzancin nasa kuma su suka xauke shi zuwa sassan duniya baki xaya. A cikinsu kuwa har da iyalansa masu tsarki.

Don haka, alaqar da ke tsakanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da

sahabbansa ba qaramar alaqa ba ce. Kuma duk wani zargi ko tuhuma ko suka ba zai fuskance su su kaxai ba sai ya shafi mai gidansu. Tuhumar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da zarginsa kuwa kafirci ne a sanin kowa.



qarqashinsu, suna madawwama a cikinsu har abada. Wancan ne rabo mai girma.

Suratut Taubah: 100

A wannan aya mutane sun kasu kashi uku. Muhajirai da Ansarai da waxanda suka bi su da kyautatawa ba da zagi ba.[3]

Mu je gaba ga wata ayar:

﴿ مُّحَمَّدٌ رَّسُولُ ٱللَّهِ ۚ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥٓ أَشِدَّآءُ عَلَى ٱلْكُفَّارِ
رُحَمَآءُ بَيْنَهُمْ ۖ تَرَىٰهُمْ رُكَّعًا سُجَّدًا يَبْتَغُونَ فَضْلًا مِّنَ ٱللَّهِ
وَرِضْوَٰنًا ۖ سِيمَاهُمْ فِى وُجُوهِهِم مِّنْ أَثَرِ ٱلسُّجُودِ ۚ
ذَٰلِكَ مَثَلُهُمْ فِى ٱلتَّوْرَىٰةِ ۚ وَمَثَلُهُمْ فِى ٱلْإِنجِيلِ كَزَرْعٍ
أَخْرَجَ شَطْـَٔهُۥ فَـَٔازَرَهُۥ فَٱسْتَغْلَظَ فَٱسْتَوَىٰ عَلَىٰ

[3] Kamar yadda Allah ya ce a Suratul Hashri bayan da ya faxi Muhajirai da Ansarai, "Kuma waxanda suka zo daga bayansu, suna cewa, "Ya Ubangijinmu! ka yi gafara a gare mu da kuma ga 'yan uwanmu waxanda suka riga mu yin imani. Kada ka sanya wani qulli a cikin zukatanmu ga waxanda suka yi imani. Ya Ubangijinmu! Lalle kai ne mai tausayi, mai jinqai. Suratul Hashri: 10

abin da zai fusata shi akan su? kuma har Allah ya yawaita yabonsu a wurare daban daban yana faxin amincewarsa da su yana sanya ma musulmi son su da darajanta su bayan kuma ya san daga baya zasu koma tsinannu daga cikin maqiyansa? Muna neman tsarin Allah daga kauce ma gaskiya.

**Wasu ayoyi kuma akan Sahabbai**

﴿وَٱلسَّـٰبِقُونَ ٱلْأَوَّلُونَ مِنَ ٱلْمُهَـٰجِرِينَ
وَٱلْأَنصَارِ وَٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوهُم بِإِحْسَـٰنٍ رَّضِىَ ٱللَّهُ
عَنْهُمْ وَرَضُوا۟ عَنْهُ وَأَعَدَّ لَهُمْ جَنَّـٰتٍ تَجْرِى
تَحْتَهَا ٱلْأَنْهَـٰرُ خَـٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًا ۚ ذَٰلِكَ ٱلْفَوْزُ
ٱلْعَظِيمُ ﴿١٠٠﴾﴾ التوبة: ١٠٠

**Ma'ana:**

Kuma magabatan farko na Muhajirai da Ansarai da waxanda suka bi su da kyautatawa, **Allah ya yarda da su kuma sun yarda da shi,** kuma ya yi musu tattalin gidajen aljanna, qoramu suna gudana a



**Ko ka san?**

Me ya sa Ahlus Sunnah suka dage akan kare sahabbai da cewa su barrantattu ne, amintattu kuma adilai?

Ka yi wa kanka wannan tambaya. Kafin kuma ka ce komai game da amsarta yi nazarin waxannan abubuwa da zan faxa maka:

**Na xaya:** Idan muka soki sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* mun buxe qofar sukar addinin kansa. Saboda me?

1. Sahabbai sun fi kowa. Don haka sukar su na bada dama ga a soke sauran mutanen kirki waxanda ba su ba. Ya suka fi kowa? Sun fi kowa domin Alqur'ani ya sauka yana bayyana matsayinsu da darajarsu yana sanar da alqawalin Allah na shigar da su aljanna. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuma ya yaba masu a hadissai da dama. Ga kuma irin dangantakar malami da almajiransa da jagora da rundunarsa da sauran nau'in alaqoqin da muka yi bayani waxanda suka wanzu a tsakaninsu.
2. Idan har Manzon da Allah ya aiko bai iya samar da al'umma wacce za ta xauki

nauyin addinin nan ta kula da shi ba kenan babu wanda zai iya wannan aiki har abada.

3. Ga shi kuma tarihi ya tabbatar da irin gwagwarmayarsu da qoqarinsu wajen kafa wannan addini da yaxa da'awarsa. An ga irin qarfin imaninsu da kyawon xabi'unsu waxanda ba a tava ganin irinsu a tarihin 'yan adam ba.

**Na biyu:** Idan aka tava mutuncin sahabbai Alqur'ani kansa zai samu cikas. Domin kuwa ta hanyarsu ne kaxai muka san Alqur'anin. Haka nan ita ma dai sunnar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba yadda zamu iya kai ga reka sai mun bi ta kan waxannan bayin Allah. Ashe ko in muka soke lamarinsu sunnah ta samu cikas kenan.

**Na uku:** Idan har maqiyan musulunci suka ce addinin musulunci tunani ne kawai da ba a iya aikatawa tun da ko wanda yazo da shi bai gan shi a aikace ba wace amsa kenan zamu ba su?

A nan ba abin da zamu ce sai dai mu roqi Allah kada ya sanya mana qunci a cikin zukatanmu da qyama ga muminan da suka gabace mu. Ya Allah ka azurta mu tsarkin zukata



muku alqawalin wasu ganimomi masu yawa waxanda zaku samu, sai ya gaggauta muku wannan, kuma ya kange hannayen mutane (kafirai) daga gare ku domin ya zama abin lura ga muminai, kuma ya shiryar da ku ga hanya miqaqqiya.

Duba yadda maxaukakin sarki ya bayyana ya san abin da ke cikin zukatansu don haka ne ya yarda da su. Wane abu ne yake cikin zukatansu wanda ya sa Allah ya yarda da su? Qarya ce da munafucci da yaudara ko gaskiya ce da tsarkin zuciya na neman yardarsa?

Wai wasu ke cewa, da farko ya yarda da su amma daga baya ya yi fushi akan su! Da wane dalili ya yi fushi akan su bayan yardarsa da ya bayyana ta cikin littafin da ake karanta shi har abada? Irin waxannan mutane ba su san girman Allah ba.. ba su san yalwantar ilminsa ba.. ba su da masaniyar cewa, Allah ya san abin da ya wuce da wanda yake nan da wanda bai riga ya faru ba idan lokacinsa ya zo ya zai faru. To, ta yaya ne Allah zai furta cewa, ya aminta da waxanda a ilminsa ya san zasu canza su zo da

﴿ لَّقَدْ رَضِيَ ٱللَّهُ عَنِ ٱلْمُؤْمِنِينَ إِذْ
يُبَايِعُونَكَ تَحْتَ ٱلشَّجَرَةِ فَعَلِمَ مَا فِي قُلُوبِهِمْ فَأَنزَلَ
ٱلسَّكِينَةَ عَلَيْهِمْ وَأَثَٰبَهُمْ فَتْحًا قَرِيبًا ﴿١٨﴾ وَمَغَانِمَ
كَثِيرَةً يَأْخُذُونَهَا ۗ وَكَانَ ٱللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمًا ﴿١٩﴾
وَعَدَكُمُ ٱللَّهُ مَغَانِمَ كَثِيرَةً تَأْخُذُونَهَا فَعَجَّلَ
لَكُمْ هَٰذِهِۦ وَكَفَّ أَيْدِيَ ٱلنَّاسِ عَنكُمْ وَلِتَكُونَ ءَايَةً
لِّلْمُؤْمِنِينَ وَيَهْدِيَكُمْ صِرَٰطًا مُّسْتَقِيمًا ﴿٢٠﴾ ﴾

الفتح: ١٨ - ٢٠

**Ma'ana:**

Lalle ne, haqiqa , Allah ya yarda da muminai a lokacin da suke yi maka mubaya'a a qarqashin itaciyar nan **domin ya san abin da ke cikin zukatansu,** sai ya saukar da natsuwa a kansu, kuma ya saka masu da cin wata nasara makusanciya. Da waxansu ganimomi masu yawa da zasu samo, kuma Allah ya kasance mabuwayi ne, mai gwaninta. Kuma Allah ya yi



da qaunar Manzo da iyalansa da makusantansa baki xaya.

**Daga qarshe..**

Yana da kyau mu lura cewa, wannan lamari ba qarami ne ba. Kuma samun rashin fahimta a cikinsa na daga cikin abinda ya kawo rarrabuwar kan musulmi. Wasu sun yi watsi da sayyidina Ali suna zarginsa da abubuwa masu girma.. *Inna Lillahi Wa Inna Ilaihi Rajiun*. Wasu kuma sai suka soke sahabbai baki xaya wai su sun rungumi sayyidina Ali ya ishe su. Wasu kuma wai basu san matsayin da zasu xauka ba. Zancen kawai! Hasken rana ai ko ga makaho ba ya voyuwa. Ga gaskiyar a fili amma dushewar basira ta sanya su a xemuwa. Allah ya kiyaye mu ya sanya mana qaunar bayinsa na gari.

Saboda haka hattara xan uwa kada wawaye su ruxe ka. Allah zai tambaye ka kai kaxai ba shamaki a tsakaninka da shi. Ina kuma ba ka shawarar ka dage ga addu'a kana mai tsarkake zuciya domin samun rahama da shiriya daga wurin Allah.

Idan hujjojin da suka gabata sun gamsar da kai Alhamdu lillahi. Idan kuma kana da saura to mu je gaba.

**Dangantakar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da Sahabbansa**

In da wani zai tambaye ka, ko Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi kaxai ya rayu? Wace amsa zaka ba shi?

Ayoyin Alqur'ani da dama ne suka sauka akan bayanin rayuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Idan ka duba su da kyau zaka tarar cewa, a ko ina aka faxi rayuwarsa da gwagwarmayarsa ta tabbatar da addini, to, sahabbansa na nan tare da shi. Bari mu duba wasu 'yan wurare kaxan domin su zamo matsayin misalai ga abin da muka faxa.

## Yaqin Badar

Allah Ta'ala ya saukar da ayoyi a Suratul Anfal akan wannan yaqin. Ayoyin kuwa sun qunshi abubuwan lura da dama. Amma zamu taqaita akan wasu daga cikinsu. Bari mu fara da wannan ayar:

قَالَ تَعَالَى: أَعُوذُ بِٱللَّهِ مِنَ ٱلشَّيۡطَٰنِ ٱلرَّجِيمِ ﴿ إِذۡ يُغَشِّيكُمُ ٱلنُّعَاسَ
أَمَنَةً مِّنۡهُ وَيُنَزِّلُ عَلَيۡكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً لِّيُطَهِّرَكُم بِهِۦ



gare shi idan ya yi azamar ya yaqi mutanen Makka. Ko wannensu ya xora hannunsa akan hannun Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* yana mai ba shi alqawalin ba zai ja da baya ba har sai ya mutu akan wannan tafarki.

Bayan haka ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya aminta aka qulla wata yarjejeniya wadda a bisa gare ta ne zai koma gida da jama'arsa ba tare da sun shiga Makka ba a wannan karon! Sahabbai suna tsananin kewar shiga Makka, musamman muhajirai daga cikinsu. Suna son gabatar da wannan ibada wadda suka baro Madina dominta amma kuma ya zama tilas su yi ladabi ga jagora, domin yana ganin abin da basu gani kuma ya san abin da basu sani ba, sannan yana tafiya ne bisa ga umurnin Allah.

Allah kuwa ya yi musu tukuici akan wannan biyayya da suka yi, ya saukar da ayoyi tari akansu in da ya bayyana masu muhimmancin wannan mataki da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya xauka da xinbin nasarorin da ke cikinsa. Haka kuma ya bayyana cewa:

tafiya aikin umrah. Ya kuwa kama hanya tare da sahabbansa waxanda yawansu ya kai dubu xaya da xari huxu (1400) daga cikin Muhajirai, mutanen Makka da kuma Ansarai, mutanen Madina.

Mutanen birni su ne suka karva wannan kira nasa ba mutanen karkara ba. Haka kuma ba munafuki guda da ya halarci wannan tafiyar sai guda xaya wanda asirinsa ya tonu da sahabbai suka yi wa jagoransu *Sallallahu Alaihi Wasallama* mubaya'a akan yaqi, mubaya'ar da aka sa ma suna *Bai'atur Ridwan* saboda Allah ya ce, duk waxanda suka yi ta ya yarda da su. Sunan wannan munafukin wanda bai miqa hannunsa ba shi ne Jaddu xan Qaisu.

Kwatanta wannan tafiyar tasu a cikin ranka, sun gangaro daga Madina suna Kabbarori da Hailala suna Labbaika a cikin sunqurmin daji wanda duwatsu sun katangance shi ta ko ina. A xaya gefen kuma mushrikan Makka sun kammala dukkan shiri na hana su shiga gari mai alfarma.

A qauyen Hudaibiyyah xin ne sahabbai suka yi mubaya'a ga jagora *Sallallahu Alaihi Wasallama* don nuna cikakken goyon bayansu



وَيُذْهِبَ عَنكُمْ رِجْزَ ٱلشَّيْطَٰنِ وَلِيَرْبِطَ عَلَىٰ
قُلُوبِكُمْ وَيُثَبِّتَ بِهِ ٱلْأَقْدَامَ ﴿١١﴾ الأنفال: ١١

**Ma'ana:**

(Ka tuna) lokacin da Allah yake rufe ku da gyangyaxi, domin (ya samar maku) aminci daga gare shi, kuma yana saukar da ruwa daga sama a kanku, domin ya tsarkake ku da shi, kuma ya tafiyar da qazantar shaixan daga ga reku, kuma domin ya xaure akan zukatanku, kuma ya tabbatar da dugaduganku da shi.

Suratul Anfal: 11

Wani abin lura kuma shi ne abin da tarihi ya tabbatas cewa, ba munafucci kafin yaqin badar. Sai bayan sa ne munafucci ya bayyana. Shi ya sa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce, yana yiwuwa Allah ya dubi mutanen badar ya ce, kuyi abinda kuke so na gafarta maku.[2]

---

[2] Sahihul Bukhari a littafin yaqoqa, babin buxa garin Makka da babin falalar waxanda suka halarci badar

Sai kuma ayar da take bayanta:

﴿إِذْ يُوحِي رَبُّكَ إِلَى ٱلْمَلَٰٓئِكَةِ أَنِّي مَعَكُمْ فَثَبِّتُواْ ٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْۚ سَأُلْقِي فِي قُلُوبِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ ٱلرُّعْبَ
فَٱضْرِبُواْ فَوْقَ ٱلْأَعْنَاقِ وَٱضْرِبُواْ مِنْهُمْ كُلَّ بَنَانٖ
١٢﴾ الأنفال: ١٢

**Ma'ana:**

A lokacin da Ubangijinka yake yin wahayi zuwa ga Mala'iku cewa, "Lalle ne Mu, Muna tare da ku, sai ku tabbatar da waxanda suka yi imani: zan jefa tsoro a cikin zukatan waxanda suka kafirta, sai ku yi duka akan wuyoyi kuma ku yi duka akan dukkan yatsunsu".

Anfal: 12

Ga wata ayar kuma:

﴿وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَهَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ
وَٱلَّذِينَ ءَاوَواْ وَّنَصَرُوٓاْ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُؤْمِنُونَ حَقّٗاۚ لَّهُم

(7/140) da Sahihu Muslim babi daga falalar badar. Hadisi na 2494.



Kuma Allah ya isar wa **muminai** (ya xauke masu yin) yaqi.

Haka dai ayoyin suka bayyana yadda Allah ya tarwatsa rundunonin kafirai ya gadar da muminai gonakin yahudu da gidajensu da dukiyoyinsu bayan da aka razanar da su aka fatattake su daga gidajen nasu. Ka kwatanta alaqar da ke tsakanin wannan runduna ta muminai da jagoransu *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Ka kuma dai sake nazarin ayoyin da kyau idan kazo tilawa a cikin wannan sura don ka gane matsayin da waxannan bayin Allah suke da shi wurin Rabbus Samawati.

## Sulhin Hudaibiyyah

Kafin a qulla yarjejeniyar da aka ba sunan Hudaibiyyah Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi mafarki, Allah ya nuna masa ya shiga Makka tare da sahabbansa sun yi xawafin xaki mai alfarma, suka yi umrah kuma suka aske gashin kansu, wasu kuma suna rarrage gashin. Allah *Ta'ala* kuma ya saukar da aya yana mai ba su tabbacin aukuwar wannan abin da Manzo ya gan shi a mafarki. Daga nan ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi yekuwar

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ٱذْكُرُوا۟ نِعْمَةَ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ إِذْ جَآءَتْكُمْ
جُنُودٌ فَأَرْسَلْنَا عَلَيْهِمْ رِيحًا وَجُنُودًا لَّمْ تَرَوْهَا ۚ وَكَانَ
ٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرًا ﴿٩﴾﴾ الأحزاب: ٩

**Ma'ana:**

Ya ku waxanda suka yi imani! ku tuna ni'imar Allah a kanku a lokacin da waxansu rundunoni suka zo maku, sai muka aika wani irin iska a akansu da waxansu rundunoni waxanda ba ku gani ba (na mala'iku). Kuma Allah ya kasance mai gani ga abin da kuke aikatawa.

Suratul Ahzab: 9

Allah ya kira su masu imani sannan ya faxi ni'imar da ya yi akansu. Idan ka bibiyi ayoyin zaka ga ko ina haka ne Jallah ya kira su wanda shi ne mafi sani ga zukatansu. Misali:

﴿وَلَمَّا رَءَا ٱلْمُؤْمِنُونَ ٱلْأَحْزَابَ﴾ الأحزاب: ٢٢

Kuma a lokacin da **muminai** suka ga qungiyoyin kafirai..

﴿وَكَفَى ٱللَّهُ ٱلْمُؤْمِنِينَ ٱلْقِتَالَ ۚ﴾ الأحزاب: ٢٥



مَّغْفِرَةٌ وَرِزْقٌ كَرِيمٌ ﴿٧٤﴾ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ مِنۢ بَعْدُ وَهَاجَرُوا۟
وَجَٰهَدُوا۟ مَعَكُمْ فَأُو۟لَٰٓئِكَ مِنكُمْ ۚ وَأُو۟لُوا۟ ٱلْأَرْحَامِ بَعْضُهُمْ أَوْلَىٰ
بِبَعْضٍ فِى كِتَٰبِ ٱللَّهِ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمٌۢ ﴿٧٥﴾﴾
الأنفال: ٧٤ ـ ٧٥

**Ma'ana:**

Kuma waxanda suka yi imani kuma suka yi hijira, kuma suka yi jihadi a cikin hanyar Allah, kuma da waxanda suka bayar da masauki, kuma suka yi taimako, **waxannan su ne muminai na gaskiya,** suna da gafara da wani abinci na karimci. Kuma waxanda suka yi imani daga baya, kuma suka yi hijira kuma suka yi jihadi tare da ku, to, waxannan suna tare da ku, kuma ma'abuta zumunta, sashensu majivintan sashe ne a cikin littafin Allah. Lalle Allah ne Masani ga dukkan komi.

Anfal: 74-75

Allahu Akbar! ka ji masu babban rabo. Duba irin shaidun da Allah ya yi akan imaninsu

cewa, muminai ne na gaskiya ba garwaye. Kuma sai ayar ta game Muhajiruna waxanda suka baro Makka don neman yardar Allah da Ansaru masu masaukinsu waxanda suka tarbi ‘yan uwansu na addini suka yi masu goma sha biyu na arziki, sannan suka haxu baki xaya suka yi jihadi don tabbatar da kafuwar addinin Allah suka karya qafafun kafirci. Sa’annan sai ayar ta sake haxawa da musulmai na baya baya waxanda da farko suka ja daga da musulmi amma Allah cikin rahamarsa ya sake kevo su suka gane gaskiya suka rungume ta suka wanke varnarsu da gyara suka yi jihadi saboda Allah a bayan haka. To, ilahirin waxannan sai luxufin Al Laxifu ya lulluve su aka riskar da su ga ‘yan uwansu musulmi magabata aka basu hukuncin ‘yan uwan juna, suka samu rabon gafara da arziki na karimci.

## Yaqin Uhud

Kimanin ayoyi 70 na Alqur’ani ne suka sauka a kan sha’anin wannan yaqi. Ayoyin kuwa sun bada haske ga dalilan faruwar wannan yaqi, da yadda ya gudana da wasu irin darussa masu muhimmanci da ya kamata musulmi su amfana



su, **kuma suka bi yardar Allah**. Kuma Allah Mai falala ne mai girma.

Ali Imran: 173-174

Duba yadda Allah ya shaida cewa sun bi yardar Allah, kuma imaninsu ya daxa qarfi. Ka lura da qarshen ayar yadda Allah ya ke bayyana yalwantar falalarsa don ka sani lalle wannan falalar sun same ta. Kaicon wanda ya ke zungurar waxannan zavavvun bayi!

## Yaqin Taron Dangi

Wannan shi ne yaqin da ake kira *Yaqin Khandaq* wanda kafiran Quraishi suka gayyato arna ‘yan uwansu daga ko ina don su gama da musulunci. Allah *Ta’ala* ya bayyana aukuwar wannan yaqi a wata sura da aka ba sunan *Ahzab*, rundunoni, in da ya bayyana halin da zukatan sahabbai ke ciki a lokacin wannan yaqi wanda aka yi shi a lokacin sanyi da iska masu qarfin gaske da irin qoqari da juriyar da suka yi a cikin wannan hali.

Mu fara da duba aya ta 9 a cikin wannan sura:

azamar dawowa amma da suka ji xuriyar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da sahabbansa sai suka arce ba sararawa ba yada zango don tsananin jin tsoro da tashin hankali. Akan haka ne Allah yake cewa:

﴿ٱلَّذِينَ قَالَ لَهُمُ ٱلنَّاسُ إِنَّ ٱلنَّاسَ قَدۡ جَمَعُواْ لَكُمۡ
فَٱخۡشَوۡهُمۡ فَزَادَهُمۡ إِيمَٰنٗا وَقَالُواْ حَسۡبُنَا ٱللَّهُ وَنِعۡمَ
ٱلۡوَكِيلُ ١٧٣ فَٱنقَلَبُواْ بِنِعۡمَةٖ مِّنَ ٱللَّهِ وَفَضۡلٖ لَّمۡ
يَمۡسَسۡهُمۡ سُوٓءٞ وَٱتَّبَعُواْ رِضۡوَٰنَ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ ذُو فَضۡلٍ
عَظِيمٍ ١٧٤﴾ آل عمران: ١٧٣ - ١٧٤

**Ma'ana:**

> Waxanda mutane suka ce masu: "Tabbas, mutane sun tarar maku (mushrikai sun juyo zasu sake dawowa), ku ji tsoron (karawa da) su. Sai (wannan magana) ta qara musu (qarfin) imani, kuma suka ce, "Allah ne ma'ishinmu, kuma madallah da madogararmu (Allah). Sai suka dawo da wata ni'ima babba daga Allah da wata irin falala, babu cutar da ta same



da su daga wannan yaqi haxi da jinjina ma sahabbai akan namijin qoqarinsu da yafe masu akan kasawarsu da basu tabbacin aljanna gidan girma.

Duba ayar farko a cikin wannan jeri. Ga abin da Allah yake cewa:

﴿وَإِذۡ غَدَوۡتَ مِنۡ أَهۡلِكَ تُبَوِّئُ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ مَقَٰعِدَ لِلۡقِتَالِۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ
عَلِيمٌ ١٢١﴾ آل عمران: ١٢١

**Ma'ana:**

> Kuma a lokacin da kayi sammako daga wajen iyalanka, kana nuna ma **muminai** wuraren da za ayi yaqi..
>
> Ali Imran: 121

Sai Allah ya fara da kiransu muminai don kawar da ko wace irin shakka game da kurakuran da suka faru a yaqin kar ayi tunanin rashin imani ya haifar da su.

Haka ayoyin suka ci gaba da bayani har in da aka zo zargin masu kuskure da laifi a cikinsu;

﴿وَلَقَدۡ صَدَقَكُمُ ٱللَّهُ وَعۡدَهُۥٓ إِذۡ
تَحُسُّونَهُم بِإِذۡنِهِۦۖ حَتَّىٰٓ إِذَا فَشِلۡتُمۡ
وَتَنَٰزَعۡتُمۡ فِي ٱلۡأَمۡرِ وَعَصَيۡتُم مِّنۢ بَعۡدِ مَآ

أَرَىٰكُم مَّا تُحِبُّونَۚ مِنكُم مَّن يُرِيدُ ٱلدُّنْيَا
وَمِنكُم مَّن يُرِيدُ ٱلْـَٔاخِرَةَۚ ثُمَّ صَرَفَكُمْ
عَنْهُمْ لِيَبْتَلِيَكُمْۖ وَلَقَدْ عَفَا عَنكُمْۗ وَٱللَّهُ ذُو
فَضْلٍ عَلَى ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿١٥٢﴾ آل عمران: ١٥٢

**Ma'ana:**

Kuma lalle ne, haqiqa Allah ya yi muku gaskiya ga alqawarinsa a lokacin da kuka rinqa karkashe su da izninsa (Allah ya ba ku nasara da farko, amma daga baya) har sai da kuka kasa, kuma kuka yi jayayya cikin al'amarin (umurnin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya bayar ga maharba su tsaya akan dutse wasu suka xauka yace a sauka in an ci nasara, wasu kuma suka ce bai ce ba, sai da yawa suka sauka) kuma kuka sava (da saukar da kuka yi) a bayan (Allah) ya nuna muku abin da kuke so (na samun galabar musulmi). Daga cikinku akwai mai son duniya (ganima), kuma



daga cikinku akwai mai son lahira (shahada da ladar yaqi). Sa'annan kuma ya juyar da ku daga gare su (sai nasara ta koma wajen kafirai) don ya jarrabe ku. Kuma lalle ne, haqiqa, (Allah) **ya yafe muku.** Kuma Allah mai falala ne ga muminai.

Ali Imran: 152

Ikon Allah! to ka gani fa. Ga laifinsu an kasa a faifai domin a nuna masu darasin da ke ciki. Amma kuma ayar ba zata dire ba sai ta basu busharar an yafe musu laifin. Manya kenan!

Daga baya kuma bayan gama wannan yaqin musulmi sun dawo jina jina, ga wahalar yaqi ga kuma juyayin 'yan uwan da aka rasa sai jibrilu *Alaihis Salam* ya zo ya ce ma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* idan kun ajiye makamai su kam mala'iku basu ajiye nasu ba, suna can sun bi mushrikai a hanyarsu ta komawa Makka. Nan take kuwa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya bada umurni, duk muminai suka zabura aka tasar ma wani wuri da ake kira *Hamra'ul Asad* domin biyar sawunsu. Kafin haka kuwa mushrikai sun yi